# TSIRRAI NA DA BAN SHAAWA

**Masana kimiya a sasssan duniya, za su kaddama da yakuwa aka fadakar da mutane akan amfanin tsirrai ga dan adam a karo na biyar.** Kungiyar masana kimiyar tsirrai ta kasashen turai ce ta dauki nauyin wanann yakuwar (European Plant Science Organization, EPSQ). Makasudin yakuwar ita ce fadakar da mutane kan amfanin tsirrai, da noma da kuma abinci masu gina jiki. Acikin yakuwar dai, an hada da abubuwan amfani da ake samu a kurmi kamar su Timba, katako, pepa da kuma tsinazirai na hada magunguna. Da kuma sanin amfanin tsirrai wurin kare muhalli.

**Gayyata.**

**Muna gayyatar kowa da kowa kama daga kan daliban** makarantan, 'yan kasuwa da shuwagabannin masnaantu. Ana bukatar hada hannun malaman jamioi da makaratun fasaha da kuma manoma. Ana bukatar hadin kan gidajen aje kayan tarihi. Allah yasa asamu nasara kamar yadda aka samu a 2012, 2013, 2014, 2015 da kuma 2017. Domin samun karin bayani latsi "FoPD Success Stories" a intanet.

**Ana gayyatar 'yan jaridu da masana kimiya da harkokin mulki** domin su tatauna akan nasarorin da aka samu a bincike binciken da akeyi akan amfanin tsirrai da kuma yadda za a karfafa cigaban sa. Wannan taron zai samu goyon bayan wasu taruruka da za ayi a dandali daban daban kamar su gareji domin kowa ya fahimci amfanin tsirrai.

**A matsayin ka na mai amfani** da tsirrai, muna bukatar a shirya taron fadakarwa ga mutanen dake kusa a ranar 18 ga watan Mayu, 2019. Burin mu shi ne a shirya taruruka da za su wuce dubu dayan da aka taba yi a 2017. Duk shekara ana shirya taron ne a ranar 18 ga watan Mayu sai dai tarurukan kan cigaba har zuwa karshen wata.

**Tsirrai na da ban shaawa.** Da ga an shuka kwaya guda, sai ka ga ya tsiro ya girma yayi ganyayyaki da yawa. Ko kuma dan karmin itace ya girma ya zama babban itace. Mutane da dabobi na amfana da haki da 'ya 'yan itacen, suna ci suna rayuwa. Ga kuma fulawoyi masu ban shaawa da kawata wuri. Masana kimiyar tsirrai sun kiyasta cewa akwai tsirrai daban daban har kimanin dubu dari biyu da hamsin a duniya. Amma wasunsu na fuskantar barazanar gushewa. Akan haka ne mu ke son mu karfafa zukatan mutanen duniya baki daya akan kiyaye tsirrai domin amfanin da ya ke da shi gare mu da kuma mutanen baya.

**Ka fadakar!**
Domin karfafa maka/ki guiwa, mun ba da damar amfanin da dandalin mu a intanet kyauta. Kana iya sauke "RP-toolbox" daga dandalin mu watau 'FoPD website'. Idan ka na bukatar dora taron ka a dandalin mu, to ka nemi ganin kodinato na kasar ku!

**#plantday**

**plantday@epsomail.org**